"Anty mardiyya Mami tana gidan su Dada ne itama?" Cewar Fatima k'aramar k'anwarsu mai shekara bakwai Zara'u me shekara goma sha biyu tace."
"Fatin mami, Mami bata nan ta yi tafiya ba yanzu zata dawo ba" Mardiyya me shekara goma sha shida. babbar 'ya a wajan Hauwa da Aminu ta kasa cewa komai, sai had'id'iye kuka take yi."
"Mardiyya" Dam gabanta ya fad'i data jiyo amon muryar Muktar wanda tun sanda abun ya faru take wasan b'uya dashi. Cak ta tsaya, Zara'u kuma ta kama hannun Fatima suka soma gaba, bayan sun gaishe da Muktar.
Gefe guda Mardiyya da Muktar suka samu, a gefen wani d'an dakali suka zauna."
"Ya k'arin hak'urinmu kuma Mardiyya?" A mugun tsarge tace.
"Mungode Allah, ina yini muktar." Idanu ya lumshe ya na jin sonta na nunkuwa a zuchiyarshi. mardiyya yarinyace mai nutsuwa da shegewa rai ta yi daram, sabida kyawawan d'abiunta da su kai mata k'awa.
"Lafiya lau Mardiyya, yaya ake ciki maganar case d'in Mami?" Kai ta sauke ta soma kuka k'asa _k'asa. Kallonta yayi cikin tausayawa yace."
"Ya isa daina kukan Mardiyya kinji ko? Dama wata magana na zo miki da shi, wanda ya dace ace kin ji tun wuri, sai dai bamu samu damar keɓewa ba sai yau. Amma ki mun uziri ba laifina bane." Da sauri ta d'ago idanuwanta sharkab da ruwan hawaye, tace."
"Iyayenka sun janye maganar Aurenmu ko, a sakamakon abunda mami ta aikata ko Muktar? Wani malolo ta had'iye mu'kut. taci gaba da ajjiyar zuchiya.
"Eh Mardiyya hakane, wallahi sun matsa akan lallai sai dai in hak'ura da auranki..." Saurin dakatar dashi tayi, ta hanyar d'aga mishi hannu, shiru yayi ya zuba mata idanu. Hak'ik'a ya gasgata son da Mardiyya take yi mishi, kuma ya gamsu da ita a matsayin uwar 'ya'ya. Amma ya zaiyi iyayenshi, da mahaifiyar Mardiyya sun sa shi a uku."
"Na ji Muktar na fahimta, Muktar bazan mutu ba in ka rabu dani. A halin yanzu nafi son in zauna in kula da k'annena in basu kariya kuma." Mik'ewa tayi ta soma tafiya ta share hawayenta tas.
"Mardiyya ki tsaya kiji dan Allah." Ko waige ta kasa yi, sai sauri take ta zubawa bata ko iya

ganin gabanta. Hannunta yayi maza ya rik'e a zafafe ta juyo tare da fisge hannunta.
"Meye Muktar. kafison kaga na sume ko na mutu sabida ka rabu dani ko? Toh bazan mutu ba, hakan ma  dama ya bani da zan ci gaba da karatuna, kuma in kama sana'a. Sadakinka ka turo a karb'ama abunka." A marairaice yace.
"Wallahi Mardiyya na bar miki duniya da lahira." Murmushin takaici Mardiyya ta yi mishi tace."
"Nagode" Tafiyarta ta yi ta barshi a wajan.
A guje ta shiga cikin gidan tana isa kan tabarmar da ta ga su Dada a zaune ta hau, ta fashe da wani irin mugun kuka mai shesshek'a. Dada ta bar kwad'on garin rogon da take yi ta ce.
"Menene ya faru Mardiyya, an yanke ma Hauwa hukuncinne? Kallon su Zara'u Dada ta yi tace."
"Zara'u d'auki kwad'onnan ku shiga ciki, ki d'iban muku naku, saiku rufema yayarku sauran. Saida taga su Zara'u sun shiga ciki sannan ta kuma duban mardiyya tace."
"Mardiyya fad'amun menene?" Cikin muryar kuka tace.
"Dama Muktar ne wai iyayenshi su ka ce bazai aure ni ba, sun fasa. Mami kuma an yanke mata hukuncin d'aurin rai da rai." Sallallami Dada ta shiga yi, tare da tafa hannayenta biyu tace.
"Ni haihuwar fulani, Hauwa ta jawo muku abun fad'en da har abada ba'a dena fad'e ba. Gaku yara mata." mardiyya ta dubi Dada tace.
"Ni Dada inaso in ci gaba da karatuna, sannan ki rok'amun Abba ko da waina in dinga toyawa a waje da yamma, domun mu d'an dinga juyawa." Hawaye Dada ta shiga zubarwa na Tausayin Aminu da yaranshi, Hauwa ta cucesu sosai."
"Mardiyya kar ki bari takaici da bak'in cikin d'a namiji da takaicin rayuwa ya durk'usar dake, ni inaso ki bar batun karatu ki fad'a koyan sana'ar hannu, ko dan ki dinga taimakama k'annenki tunda kinga Abban ku bashi da hali sam, ni abunda nake so kenan amma sai abunda kika ce." Mardiyya ta share hawayenta. bakinta na yi mata d'aci tace."
"Dada na d'auki shawararki wallahi, kinga su Zara'u sa samu su ci gaba da karatu in Allah ya so, amma wainar ma inaso in soma toyata zuwa gobe." Dada sai lokacin ta d'anji sanyi a ranta tace."
"Gobe kuma? Ai dole sai da jari Mardiyya. a k'alla kina buk'atar nera dubu uku kafin ki soma toya waina, tunda kinga za'a sai shinkafar tuwo ga cefanen kayan miya, ga kuma su itace da man suya, ai sai mun had'a kud'in mardiyya."
"Dada Muktar yace ya bar mun sadaki halak malak harma na yi mishi godiya, ki bani dubu uku zuwa yanma inyo cefanen komai da komai sauran ki ba Abba yayi amfani dashi." Dada tace.
"wayyo Allah Mardiyya Allah yayi albarka kinji, Allah ya sanya muku salama da juriyar rashin Hauwa. Wancan d'akin saiku gyara ke da k'annenki kuma saiku dinga kwana. Abbanku kuma zai koma shagon waje da kwana, Allah ya k'ara rufa asiri, kece babba mardiyya ki duba k'annenki domun yanzu kallon uwa zasu dinga yi miki , duk da dama kece ke ɗawainiya dasu, tun ƙarfinki baima kaiba. Amma yanzu dai ba Hauwa, tunda a kurkuku zata ƙarashe shingin rayuwarta, sai kin cire damuwa a ranki tukunna. Gashi 'yan uwan gyatumar taki suma fama suke yi da kansu wannan rayuwa sai dai godiya kawai, taso muje in taya ki gyaran d'akin. Dada da mardiyya  suka gyare d'akin tas su ka sanya wani cinyayyen labule da wata guntuwar tabarma. mardiyya ta fice zuwa shagon waje dan gyara ma Abbansu nashi d'akin, cikin awa guda ta tsabtace ko ina ta shinfid'a mishi zanen gado a katifarshi mai kamar tabarma. Kullo shagon ta yi ta shiga ciki. Alwala ta yi sannan ta shiga d'akin Dada, tarad dasu ta yi duk suna Allah. itama tada tata sallar tayi. Bayan sun idar Dada tace.

"Mardiyya ki ci kwad'on naki ni zan fita zamu je barkar haihuwar shatu ni da gwamma, in yaso na ari kud'i a wajan gwamma in yo miki cefane ko tunda ta cikin kasuwa zamu ratsa. Mardiyya tace.
"Yauwa Dada kinga na huta shikenan. Sai kun dawo." mai Dada ta shafa ta sake saka kwalli ta d'auki mayafinta ta fice."
"Anty Mardiyya anan gidan zamu zauna kenan har da Abba?" Zara'u ce ta yi mata tambaya, Fatima kuwa tsakar gida ta fice ta na ta wasanta abunka da yaro.
"Eh Zara'u kinga Abba ya samu damar sanya matar da zai aura acan kinga ya samu sauk'i."
"Toh yaushe zai kaimu wajan Mami kuma?"
"Toh Zara'u Mami yau aka tafi da'ita, kuma kinga sun je dubata yau, sai dai in zai kuma zuwa sai ku bishi kuje tunda kunason ganinta." Hawayen bak'in ciki da takaici mardiyya take zubarwa data tuno sanda Hauwa ta zubar dasu ta mance dasu, bata ko ji tausayinsu ba, balle ta ji na Abbansu."
"Ke bazaki je ba ko Anty?." Mik'ewa Mardiyya tayi ta fice. tsintsiya ta d'auka ta soma sharar dole. Sai da ta share gidannan tsab, ta kuma wanke band'akin gidan. Wanke _wanke ta tattarema Zara'u wacce take zaune a dokin k'ofar Dada ta yi tagumi."
"Zara'u zo ki yi wanke wankennan maza. Ni kuma bari in gyara ma Dada d'akinta.

JACARA
"To yanzu menene shawarinku akan gadonnan da za'a raba muku, na mahaifiyarku da mahaifinku?  ni shawarar da zan baku kusa haya a gidanku gadon mahaifinku, ko wacce tana d'akin mijinta tana karb'ar hayan abunta tasan duk shekara tana da kud'i da zasu shigo mata. Tunda gidan Hauwa ta gyara muku shi, zaku iya samun d'akuna guda guda. Ɗan abunda aka raba aka baku gadon Marne kuma, sai ku gagganɗa kuyi wani abun." Nanne k'anwar mahaifiyarsu Hauwa ce take ma su Hafsat bayani" Ummu tace."
"Hafsa, Sameerah,  ku da sauran ƙannen naku. Ni abunda zan fad'a muku lokaci yayi da zaku rungumi mazajenku kuyi musu biyayya dolenku, domun kunga ishara akan mahaifiyarku mai rasuwa. da ma Hauwa, dan haka ruwa cikin cokali ya ishi mai hankali yai wanka. Ku nutsu sosai ku yi zaman aure me kyau. Nanne kuma ta fad'a muku gaskiya, karku siyar da gidanku na gado, ku xuba haya kuna d'an amsan abunda ya samu 'dan gadon mahaifiyarku kuma da zaku samu sai ku ja jari da shi ku kama 'yar sana'a, tunda kunce har mota ta siya, mu dai mun yafe, ku d'in dai ta taku muke yi koba gaskiya ba?.  lokaci yayi da zaku xubar da makaman yak'inku, ku daina azabtar da mazajenku zaifi muku. Ku ji da abun kunyar ma daya faru daku wanda k'ila da ba dan kun jima da yin auren ba, da ba mai auranku ma, Hauwa ta ja ma mutane bala'i da masifar da har abada da wannan ciwon zan koma ga mahaliccina, kuma babu mahaukacin da zai auri 'ya'yanta dai." Haka su kaita tattauna matsalolin da suke ciki, a wannan lokaci."

Aminu
Tafiya kawai yake yi a k'afa da yaga tafiyar k'afa ba zata kaishi ba,sai ya tare abun hawa ya hau, a daidai k'ofar gidan mai adashen gata ya tsaya, yaro ya aika yace ai mishi sallama da mai adashen gata. Bata d'au loaciba ta fito.
"Aminu kaine a tafe?"
"Eh nine d'ari zaki d'an bani in sallami mai mashin tukunna." Lalitarta ta bud'e ta zaro d'ari ta

mik'a ma Aminu, amsa yayi ya sallami mai mashin d'in kana ya dawo."
"me adashen gata, dama zuwa na yi in amshi kud'ina da nake zubawa amma rabi, rashin lafiya ce ta taso a family kuma kowa ba kud'i kinsan garin sai adda'a." Mai adashen gata tace."
"Babu komai Aminu ai amfanin ajjiyar kenan ita dama ajjiya dad'i gareta, bari in baka nera dubu sittin da biyar kenan zan baka ko? kace rabi." Aminu yace.
"Eh haka zaki bani." Gida ta koma bata jima ba, sai gata da kudin ta bashi, bai ko tsaya kirga kudin ba ya xura a aljihu ya wuce, kai tsaye ya koma asibiti ya je ya siyo allurannan da magunguna. sai da ya kashe dubu ashirin  da uku da d'ari biyu.
Da sallama ya shiga cikin d'akin, Hauwa har zuwa lokacin tana bacci bata farka ba, Jamila tana zaune ta zuba uban tagumi, Baffa kuma yana tsaye yana kallon Hauwa. ga gandirobobi guda biyu a gefe da gefen gadon."
"Aminu ka dawo?"
"Eh Baffa na dawo, bata farka ba ko?" Jamila ta sauke ajjiyar xuchiya tace.
"Bata farka ba, d'azu dai ta bud'e idanta sai kuma ta rufe. Likita dai yanata shigowa dubata." Shiru Aminu yayi yana kallon fuskar Hauwa cike da tausayinta."
"Bari inje in kai mishi magungunan, daga nan zan d'anje gida da yamma zan dawo kafinnan ta farka." Baffa yace.
"Allah yayi albarka Aminu wai duk tsiyar da Hauwa ta tabka amma baka gaji da hidimta mata ba, sannu Allah ya baka mace ta gari wacce tasan mutuncinka. Nima zan tafi gida dan akwai malamai masu rabon gadon ita uwar tasu, da na mahaifinsu da ba'a rababa,  za su zo kar suita jirana ba dad'i Jamila za'a aiko da abinci anjima." Tare Aminu da Baffa suka fice, Aminu saida ya kaima Dr magungunan da alluran kuma ya shaida mishi zai je ya dawo zuwa yamma. Dr yace.
"Dama ka bari sai zuwa gobe sai ka dawo dan bazata farka yau ba sai zuwa gobe, dan wannan allurar da zan k'ara yi mata zata kuma sata baccine."
"Toh shikenan likita mungode." Sallama yayi mishi ya fice. Kai tsaye zuwa galadanci."
Mardiyya suna tsakar gida ita da k'annenta sai tunano Muktar take yi da irin son da yake yi mata, amma gashi lokaci d'aya mahaifiyarta ta ruguje mata farin cikinta. Sallama su ka ji ana dokawa daga k'ofar gida, mardiyya ta zari mayafi ta le'ka. Abokin Abbanta ta gani Saminu a tsaye.
"Sannu da zuwa Abba, ina yini?" Kallon mardiyya ya ke yi cike da tausayawa ya ce."
"Lafiya lau Mardiyya ya k'annenki?" Kanta na k'asa tace.
"Lafiyarsu k'alau Abba, ina su Murja?" murmushi yayi yace.
"Mardiyya ta Murja, Dada fa?.
"Ba ta nan ta fita barka" Kai ya kyad'a yace.
"Toh mu shiga daga ciki." Juyawa ta yi ya bi bayanta, sai k'arema takunta kallo yake yi. Fatin Mami tana hangoshi ta zuro da gudu ta d'aneshi tana  dariya."
"Abba kaine?" Sake rungumeta yayi a jikinshi yaima kanshi masauki a tabarma kusa da Zara'u." Zara'u tace
"Abba ina wuni?" Kanta ya shafa cikin kulawa  ya amsa gaisuwar tata, sannan ya dawo da dubanshi ga Mardiyya yama kasa d'auke kai. Duk d'agowar da zata yi sai sun had'a idanu hakan duk sai ya takurata. ba tun yau ya saba yi mata haka ba, kullum in yaje gidansu a cikin kallonta kawai yake, haka in ita ce  taje gidanshi wajan Murja 'yarshi kuma aminiyarta sai yaita

kallonta ita ta rasa dalili.
"Mardiyya! Muktar yaje wajan aikina a kasuwa, ya sanar da ni yanda iyayenshi suka kafe kan lallai basu amince ya Aureki ba. Ki yi hak'uri in sha Allah wanda zai b'ullo miki ya fi shi alkhairi kuma ya fishi sonki. Mahaifiyarki ki bita da adda'a kawai dan ta jefa kanta a cikin mummunan hali.
Hawaye Mardiyya take yi sosai da sosai. Da sallama Aminu ya shiga cikin gidan nasu. Duk yaran suka nufoshi dan yi mai sannu kamar yanda su ka saba. Tsabar son su da tausayinsu ji yake yi tamkar ya maida su ciki ya huta. Fatin Mami ya d'auka a kafa'darshi, cikin dariyar yak'e yake yi ma  Amininshi Saminu magana.
"Kai kuma anan ka fake ko ka je nema na?" Zama yayi a kusa da Aminin nashi, mardiyya kuma ta ja k'annenta suka shige ciki."
"Saminu zuchiyata har  gaban abada ba zata iya daina son Hauwa ba. Ni nasan a cikin k'unci zan rayu har abada, kamar yanda Hauwa zata kasance a gidan yari. Yanxu haka fa tana asibiti hawan jini ya kamata, zuchiyarta na shirin kamuwa da ciwo. Kasan Allah ni Auran ma da zan yi na fasa Saminu." Sororo Saminu ya shiga kallon Aminu, ranshi ya matuk'ar b'aci sosai.
"Ka sani in ka fasa Auren Lubabatu a gaskiya ka yaudari xuchiyarta kuma ka cutar da ita. Ita Hauwan lokacin da taso canji bata canja maka bane, dad'in Aure da Hauwa ai kai kanka kasan babu meye matarnan ba taima  a rayuwarka ba Aminu. Duk bala'in data hurgaka a ciki amma har yanzu ka kasa dena sonta? Amma Allah ya tsine wannan soyayyar." Aminu wani irin zafi zuchiyarshi take yi mishi mai wuyar fassara, shi kanshi yakan zauna yai tunanin shin wanne irin so ya ke yi ma Hauwa Alhalin yasan ba sonshi take yi ba. Wanne irin azabtar da shine Hauwa bata yi ba? Shi kanshi bazai iya k'irga sau nawa Hauwa ta hanashi bacci ba. Amma kuma yana tuno soyayyar ta mai wuyar goguwa. soyayya mai sanyi.Idanu ya lumshe yama rasa me zaice ma Amininshi dan ya fishi gaskiya."

*TALLAH*
Ina kuke amare uwayen gida kai har ma da ƴan mata? Ko kun san Mrs Bukhari mai kayan ƙamshi, ai in dai batu na kayan ƙamshi gyaran jiki da na ɗaki to kai tsaye ku  ne mi Badi'at domin gwana ce ta ko wanne fanni a ciki. "Wai ƙamshi kina nufin Badi'at dai marubuciyar nan tamu mai nishaɗantar da mu?"
"Tabbas Fati ita take magana, ai kin dai ji yadda ake magana a kai na, hatta me gidana ya jinjinawa Badi'at domin duk wani ƙamshi da zaki ji a jikina tare da gidana to daga ita ne, ke me kankat ma har gyara na nake yi domin gyaran aurena daga gareta ne, shi ya sa bana wasa da gyaran jikina da na gidana har kuke kirana da ƙamshi."
"Eh tabbas nima na jinjina mata, kuma zaki bani addireshinta domin nima na kwankwati wannan garaɓasa. Ko zaki iya faɗa mini abubuwan da take sayarwa.?"
"Bari na faɗa miki akwai...

Humra
Kulacca
Sudanese Humra
Kulacca ta gashi.
Turaren wuta ɗan gaske, iri daban daban.

Turaren mopping
Room freshner
Turaren turara kaya.
Turaren wuta na toilet
Sannan akwai ingantaccen maganin infection
Ina da magungunan mata, wanda zai gyara amarya da uwar gida.
Wanda zasu shiga daga ciki kuma
Akwai sabulun amare, da dilka ta amare, wanda zaisa amarya ta fito ta haska tas
Kabbasa
Setin kujerar tsugunno
Sannan inayin turaren wuta da kasko, da ashana wanda ake rabawa a taron biki ko suna.
Ina bayar da sari.

Ma sha Allahu to taya zan sameta domin mallakar nawa?

"Kai tsaye zaki mata magana ta whatsApp ko kiranta ta wannan number.

08179523215

*TALLAH*
A yau nazo muku  da manya manyan magunguna domin gyaran Auranmu! Saboda yadda zamantakewarmu ta AURE keta kara tabarbarewa. Mata iyayenmu ku fito ku gyara jikinku , domin wallahi har Abadan macen da bata gyara bata isa ta hada kanta da mace me gyara ba har abadan! Mu gane yaku yan uwana mata, ma'aurata! wallahi gyara shine mace Akwai mata dayawa dasuka san magunguna na, a online Suna siya kuma Alhmdulillahi ba wadda ta siya bata dawo tamin godiya ba, Alhmdulillahi!Alhmdulillahi! Alhmdulillahi! Yawancin mata dayawa na nemana ta dayan sim dina sede nayi losing dinsa sede wannan shi yake Aiki 08104335144, A YAU NAZO MUKU DA MAGUNGUNA INGANCI DA IZININ UBANGIJI, WATO AINIFIN HADI Iri ~iri na MALLAKA D'ANA MIJI ALFARMAR ANNABI SAW, ina tabbatar muku da magunguna na babu shamaki base na tsaya bata lokaci a bayaniba zanso ku gwada dan tantance GASKIYA * Akwai cututtukan dake hana maganin mata aiki idan kinason sani ki tuntubeni ta wannan lambar 08104335144 wadannan cututtukan inhar kinadasu wallahi duk maganin daza kisha bazeyi Aiki ba, kuma bazaki taba fahimtar komiba a harkar dadih na magungunan mata.

*MUNADA MAGUNGUNA AVAILABLE KAMAR HAKA*👇🏾

*ingantaccen maganin infection *

Ingantaccen maganin basir

Ingantaccen maganin gyaran nono

Ingantaccen maganin gyaran hips

Ingantaccen maganin kara kiba kiyi dumur~mur dake

Ingantaccen maganin rage tumbi  meyi tsakani da Allah

Ingantaccen maganin matsin  farji mesa dadin farji ga azzakarin d'ana miji.

Ingantaccen MALLAKA TA DOMIN ALLAH (Bata harkoki) shine sunansa, hmmmm Wannan magani inada tabbaci a kansa shidin hadine kawai na mallakar d'ana miji akwai komi a cikinsa na mallaka hajiya ki gwada kisha mamaki Alfarmar Annabi SAW.

Se matsin (GAMADIDI) wannan matsi in kikayi amfani dashi har abadan abidina mijinki baze kawo a gaban wata ya mace ba in har ba gabanki bane wannan inada tabbaci a knsa 💯 kuma wadanda suka saya ma sun kara tabbatarmin da kyaunsa na mamaki.

Akwai zallan hadi na amarya

Akwai hadi na uwar gida sarautar mata wannan seat ne akwai komi a cikinsa.

Akwai ingantattun gumba iri iri kamar haka 👇🏽

Akwai gumbar Madara
Akwai gumba me rubutu 🤐
Akwai gumbar kankana
Akwai gumbar giginya (sa megida kuka)
Akwai ingantacciyar gumba me suna (BARIN MAKAUNIYA)
Akwai gumbar hasi
Akwai zallar gumba wadda ita ta rubutuce zallarta zaki ganta baka karki damu Aikin kawai zaki duba 😉
Akwai gumbar gero
Akwai gumbar ridi
Akwai gumbar garin gamadidi  ita ta mallaka ce zallarta.🤐

Akwai tsumi iri iri sunansu sha yanzu magani yanzu 💯👇🏽

Akwai tsumin kankana
Akwai tsumin baure
Akwai tsumin rubutun Ayar Allah
Akwai tsumin kwakwa
Akwai tsumin giginya
Akwai tsumin GORON SUDAN (wannan special ne dan kudinsa ma daban yake)
Akwai ingantattun magunguna na tada shaawah kama daga na turawa har zuwa na Islamic

wato namu na gangajiya. Akwaifa maganin maza madam na hausa dana turawa 😉 duk basuda side effects 👌

Akwai rubutun mallaka
Akwai zoben mallaka
Akwai hayakin mallaka
Akwai zani na mallaka
Akwai hadin ci da kaza
Akwai hadin yan shillah
(Muna dafa kaji da yan shillar ma dade sauran abubuwa da dama,)
Akwai dambun nama na mata wanda ke dauke da magungunan sirri na mata mesa tsantsi da laushi da ruwa a farjin mace 😉

Akwai magunguna na ban mamaki wadanda base na rubutasu ba saboda SIRRI 😉
Muna aika magungunan mu kasa kasa gari gari *UWAR GIDA KI GARZAYO QUEN SANAF Islamic chemist kise magunguna na ingantattun ne insha Allahu kin wuce takaicin d'ANA MIJI * direct to me 08104335144 muna sauraron masu shawarwari a kan zaman AURE insha Allahu, amma in knsan baki shirya siyan magungunan jima'i ba na mata ko na maza pls karki kirani.

_Ummu Maheer_
*DINYAR MAKAHO*

_Miss Hajo_
*KHADIJATUL SABREEN*

_Mrs Bukhari_
*ANGULU DAKAN ZABO*

_Ummu Affan_
*SANDAR MAKAUNIYA*

_Mom Islam_
*TSAUTSAYIN TAUNA*

*Ga tsarin yanda biyan yake*

_Guda d'aya 300_
_Guda biyu 500_
_Guda Ukku 700_
_Guda hudu 800_
_Guda Biyar 1k_

Kai tsaye zaku iya turo kuɗinku ta wannan hanya.

0037219728
FATIMA RABIU SUNUSI
StanbicIBTC BANK

Shaidar biya ta nan

0810 433 5144

Masu turo kati MTN ta wannan number.

0702 616 6536

Ƴan Niger zaku turo da naku kai tsaye ta wanna number.

0706 860 6171

*Mun gode da kasancewa da gawurtattu biyar taku na biyu* 🤘🏿

mrs Bukhari ce
[09/12, 19:49] Badi at: GAWURTATTU BIYAR
DAGA ALK'ALAMIN
BADI'AT IBRAHIM
MRS BUKHARI (B4B)

*ANGULU*
*DA*
*KAN ZABO*
5/6
"Aminu ka yi hak'uri da fishin dana d'auka, Hauwa uwar 'ya'yanka ce dole ka mutuntata. Amma nazo maka da maganganu biyu, wanda bansan tunanin za zai zo kanka ba in na sanar da kai ba." Zama Saminu ya gyara sannan ya d'aura da cewa."
"Muktar ne ya zo ya same ni a kasuwa, yake sanar dani cewar iyayenshi sun ce wai bazai auri Mardiyya ba, sakamakon Abunda Hauwa ta aikata. Kuma yace ya yafe sadakinshi ya barma ita Mardiyyan, sabida kyautatawa. hakanne ya bani dama nace bari in yi amfani da wannan damar in gabatar maka da kaina a matsayin manemin mardiyya mai neman auranta, izinin zuwa zance zaka bani, ni zan zame mata gata, mijin rufin asiri." Ajjiyar zuchiya Aminu ya sauke, ya runtse idanunshi yana saurаron bugun zuchiyarshi wanda ta tsinke yanzu. Yafi kowa sanin waye Saminu, mutumin kirki ne Aminin arziki. Amma kuma yasan iyalinshi bata da mutunci, kuma bata daraja Saminu, sannan Saminu mai k'aramin k'arfine sosai, dakon kaya yake yi a kasuwa, mata biyu basu kamace shi ba sam, in yace bai amincewa Saminu ba kuma, ta yuwu ya

fahimceshi, ta yuwu yai mishi fassara mara kyau, kanshi yayi zafi, gashi ya fi son ya aurad da Mardiyya da wuri, dan tsoro wannan duniyar take bashi. Amma ya rasa wacce amma zai yi amfani da ita ga Aminin nashi, nisawa yayi.
"Saminu yanzu abunda nake so da kai shine ka d'an bamu lokaci daga ni har Mardiyya, yanxu muna cikin wani yanayi na damuwa da son kad'aici. Amma ba zai gagaraba Abokina." Ajjiyar zuchiya Saminu ya sauke ranshi fari fat kamar audiga. Wayar Aminu ce ta soma ruri, Lubabatu ce ke kiranshi, yau kwana uku cikakku basa waya, kuma yana ganin missed calls d'inta barkatai da messeges d'inta. Bashi da nutsuwa sam da zai iya ara mata lokacinshi, bikinsu saura kwana tara ya rage. Idanu ya kuma lumshewa yana mai da numfashin daya jawo cikin huhunshi, Saminu ne ya d'auki wayar.
"Assalamu Alaikum Amarya bakya laifi ko kin kashe 'ya'yan masu gida." Daga cikin wayar Lubabatu tace.
"Saminu ni kam lafiya laifi naima Aminu daya shareni ya dena d'aukar wayata, ko dai dan abunda ya faru da tsohuwar matarshi ne?" Saminu yace.
"Lubabatu da farko zan soma da baki hak'urine, domun tun ranar da abun ya faru ba mu zauna ba muna ta cuku cukun ganin an gama shariar, toh kinga an kammala komai, ayi hak'uri dai." Murmushin takaici kawai ta yi tace.
"Dama Mama ce tace in sanar muku suna so su zo jere, gobe toh shine tace in kira." Zufa ce ta karyo ma Saminu, sai da yai nadamar d'aga wayar ma baki d'aya.
"uhm Lubabatu, za mu zo dai gidan zuwa dare koma me ake ciki zaki ji, amma akwai d'an matsala ne."
"Matsala sabida tsohuwar matarshi ko? Dama ai nasan za'a rina. k'it ta kashe wayarta.
"Hello Hello Lubabatu!!! Shiru.
wayar ya sauke yace.
"Abokina na rok'eka da girman Allah kar a d'aga wannan bikin ka daure, nasan a rashin uwa ne za'ayi uwar d'aki, kuma a halin da kake kad'aici bai kamaceka ba, yaushe ka rabu da deepretion yanzu gashi zaka kuma haifarma da kanka wata damuwar, nayi imani da Allah da za'ayi ma gwajin zuchiya yanzu haka k'ila a samu bata watsa jini a gangar jikinka yanda ya kamata."
"Saminu ina gudun in kasa ba Lubabatu lokacin da zata buk'ata a gareni ne. bana son in shiga hakkinta. Babu wata nutsuwa a tare dani, wanne aure ne? ni na fasa."
"Ah wallahi baka isaba, aure ba fashi, kar ka yi ma yarinyarnan haka Aminu." Harararshi Aminu yayi yace.
"A d'aga toh, in samu in d'an warke, kuma yarannan kulawata sukafi buk'ata a halin yanzu."
Dada ce ta shigo hannunta rik'e da bak'ar leda. Da sauri Saminu ya je ya karb'ota.
"Sannu Dada kin dawo?" Mayafinta ta cire ta rataye a igiya. Sannan ta zauna a dokin k'ofa tace.
"Nadawo Saminu kazo gun abokin naka ko? ai gara ka taya ni yi. na rasa da me Hauwa ta lashe mai zuchiya haka, dubi yanda ya rame ya fice a haiyacinshi, yaushe muka gama jinyarshine ne, so yake Hauwa ta kashe shi ma huta duka dallah" Saminu yai gyaran murya yace.
"Dada ayi hak'uri dai ai duk k'ulafucin Hauwa da yake yi dole ya barta, tunda a gidan d'an kande zata idasa rayuwarta. Duk abun ƙyamar data aikata. shi nemo mayafi yake yi a shirinshi na lullub'e mata aibi.
"Da nasan haka aurannan zai zame mana jaraba da sam ban amince mishi ba wlh tun farko,

wacce wahala ce bai sha ba tun neman? Ashe da gaskene da akace matan shuwa mallake miji suke yi. Gashi ta jefa rayuwar yaranta mata cikin garari, har Muktar ya fasa auran ita mardiyya, kuma wallahi basu da laifi, bak'ar uwarta ce sila." Saminu yace.
"Dada ayi hak'uri dai wannan lamari babu dad'i. Lubabatu ta kira tana sanar da mu iyayenta suna son su yi jere zuwa gobe. Dada tace.
"Toh babu laifi ai, fenti za'aima d'akin kawai. adashen kayan akwati da yake yi a wajan mai adashen gata kuma. zanje in yi magana da ita zuwa goben saita had'a abunda ya samu,  Allah ya  sa a dace."
"Dada ni sai nake ganin kamar a d'an d'aga bikinnan ko da wata biyu a k'ara, kinga yanxu d'an aikin dana dogara dashi babu, shagonma an rufe, inaso dai in soma bin Saminu kasuwa in sha Allah, toh sai nake ganin sake wannan gidan zanyi kawai, kud'in hayar gidan dubu tamanin ne, kuma yanzu bani da halin biyan hakan." Dada ta yi shiru tana nazarinshi da kyau, tabbas ita uwace mai son ganin 'ya'yanta a cikin walwala, bata fatan Aminu ya kuma shan wahala akan mace kamar yanda ya sha a baya.

"Ku na ji ko Saminu, Aminu?" da
"Eh" suka amsa mata
"Aminu ka daure ka auri Lubabatu, karka fasa, nasan kana cikin halin damuwa dole. Ni zan koma wancan d'akin da Mardiyya ta gyara musu, inda zan fitan tunda ciki biyu ne sai a yi fenti da gyaran silin ita Lubabatun sai ta zauna anan. In dinga ganinku kusa dani d'in ai yafi mun. Can d'in sai ka sake. dama can yafi k'arfinka 'yar gwalce ta matsa nan d'in take so. Ala tilas Aminu ya amince ma su Dada kan abinda su ke so.
"Mardiyya na son ta kama sana'a dan dogaro da kai masa zata soma toyawa da miya na siyarwa, amma tace in tambaya mata kai."Murmushi yayi kawai yace.
"Masa kuma? Mardiyya rigima, toh sai abunda kika ce Dada." Dada tace.
"Ah ni kam na amince kaga harna siyo mata cefane, nera dubu uku tace in kazo ka bata, a cikin kud'in sadakin muktar dan yace ya bata duniya da lahira, shauran kuma tace ka rik'e. A aljihu yasa hannu ya ciro dubu shida ya mik'ama Dada.
"Gashi Dada, ki bata dubu hud'u, dubu biyun kuma kwa yi cefane. Bari mu je can gidan mu kwaso kayan su Mardiyya. Daga nan sai a siyo fenti."
"Toh Allah yayi Albarka."
"Ameen Dada" Sallama Saminu yai ma Dada, sannan suka fice sai gidansu inda Hauwa ta zauna. Motar kaya suka hayo ta kwashe musu komatsan tsunmokaransu, daga nan suka siyo fenti da siminti, kana suka dawo gida.
Da kyar Aminu ya daure ya sha kunu mai zafi, Fatin mami tana jikinshi sai surutai take yi mishi,shi kuma yayi jigum yana tunanin rayuwa. Saminu kuma yana cikin d'akin Dada da suka gama kwashe kaya. 'Yan ramukan b'era ya tottoshe,yayi ciko a k'asa inda plastan ya farfashe, sannan yai fenti, duk shi kad'ai.
"Saminu ka gama?" Saminu da ya fito duk ya had'a xufa yace.
"Na fito, lokacin Sallah yayi mu je masallaci." Tare su ka je masallaci su ka yi sallah, da yamma kuma Saminu yasa Aminu a gaba zuwa gidansu Lubabatu.

Anguwar kurawa

LubabatuTana k'ofar gida gaban bokitin fentin kunun gyad'a dake gabanta, ga Alala cikin k'atuwar kula, samari sun baibayeta anata siya. K'awarta Amira tace.
"La Lubabatu ga ango fa da wannan abokin nashi, maza jeki bari in sallami jama'a. Da sauri Lubabatu ta mik'e tana yak'e, Tahowa tayi inda suka zauna a dakanin gidan nasu.
"Assalamu Alaikum" Saminu ne ya amsa mata. Aminu kuma da ido ya bita kawai. Waje ta samu ta zauna da ladabi ta gaishesu. Lubabatu yarinya ce d'anya dan da kad'an tafi Mardiyya shekaru. Amma ita mai garin jiki ce, dan ta na da k'iba, hakan yasa ta cika ido.
"Lubabatu kiyi hak'uri da rashin jinmu da ki ka yi, wallahi al'amuran dai ke kinsan komai, toh amma yanzu an gama case d'in duka." Lubabatu tace.
"An yanke mata hukunci kenan Saminu?" D'an yamutse fuska Saminu yayi yace.
"An yanke mata d'aurin rai da rai, amma yanxu haka tana asibiti tana jinyar hawan jini." Wani irin dad'ine ya lullub'e zuchiyar Lubabatu. A fili kuma sai tace."
"Kai amma abun baiyi dad'i ba gaskiya." Aminu ya dubeta yace.
"Ya su mama, ya shirye _shirye kuma?" Kallonshi tayi da soyayya tace.
"Shiri ana ta kan yi, saura k'iris in zama mallakinka." Murmushi yai mata mai burgewa yace.
"Kina farin ciki kenan?" Far tayi da ido tace.
"Sosai ma. Inda kake  nan za'ayi jeren ko?"
"A'a Lubabatu, a gidanmu zamu zauna, kinga yanzu bana aiki tukunna, duk da zan soma bin Saminu kasuwa, amma dubu tamanin ina na ganta yanzu ai da yawa. Ki fad'a musu a can gidanmu za'a kai kayan." Shiru ta yi, ita da take shirin b'alle amarci da rayuwar shagwab'a ya zai ce mata tare da mayaifiyarshi zata zauna, bayan gida guda ɗaya ne tak a  gidan, ita da take da burin ta dinga wanka da mijinta tare harma da irin wasan soyayya na guje gujennan. Amma da yake Lubabatu yarinya ce mai shegen wayau da kissa irinta yaran zamani sai tace."
"Nima zan fi so in zauna kusa da Dada, da yarana ko dan in samu ladansu duka. Aminu yaji dad'in batun Lubabatu, hakanne yasa har ya saki jiki da ita su ka tab'a hira. da zasu tafi ta d'ura musu kunu cikin gorunan swan manya, ta xuba musu Alala kowa da kwanonshi, ta sama kowa a leda, ta d'akko dubu biyu ta basu kud'in mota."

Jacara
Malaman da zasu rabo gadon su Jamila ne suka iso, suna tsakar gida an shinfid'a musu tabarma. Baffa bai jima ba ya iso, Hafsa ce ta kawo takaddar da suka rubuta duk wata kadarar da mahaifiyarsu ta mallaka,  mahaifinsu gida ya bari shine wanda suke ciki. malamai suka gama ganin komai su kai ma komai kud'i.
"Toh zamu raba gadon yanxu, tana da 'yan uwane na jini ita mai rasuwar?. Malam ne yake tambaya, Baffa yace.
"Ta na da k'anne wanda suka fito ciki d'aya su biyu, ga su nan, amma kuma iyaye basa raye. dangi duk basa raye, sun d'an fad'a iftila'in boma bomai da su kaita tashi a Borno, da yawan danginsu ta wannan hanyar suka mutu, sauran kuma lokacine ya cika. Nanne tace.
"Ni da 'yar uwata bamu da buk'atar gadon 'yar uwarmu, a rabe ma yaran kawai. Baffa yace.
"A'a nanne, ke dai ki bari a baku, in yaso kwa basu da hannunku. malam yace.
"Toh ita Hauwa an cireta a cikin wannan lissafin domun bata da gadon mahaifiyarta sam. Nan malam ya shiga rabo, tsab aka raba aka ba kowa nashi. Hafsa jikinta ne ya shiga kakkarwa da ta ga wata sark'ar gwal wanda ta tuno tabbas ta san sark'arnan toh me sark'ar take yi a wajan

mahaifiyarsu? Bata da mai bata wannan amsar, amma kuma ta had'iye mamakinta da d'aura d'amarar bincike tuk'uru har sai ta gano bakin zaren. Da yamma kowa ya watse ya nufi gidan Auranshi."

Saminu
Da sallama ya shiga cikin gidan nashi. Yaranshi suka nufoshi da gudu.
"Baba Baba Baba." Farida tana gaban murhu ita da Murja babbar 'yarta k'awar Mardiyya, tuwo Farida take tuk'awa, Murja na warwara mata gari. Kawar da kai ta yi akan Saminu tare da had'e rai. Murja tace.
"Sannu da zuwa Baba"
Kujerar tsugunno ya ja tare da zama, Aminu takwaran amininshi na mak'ale dashi, hancinshi duk majina."
"Yauwa Murja, zo ki d'au Aminu a share mishi hanci." Farida dai bata ko sake kallon inda ya ke ba, sai tuwanta take tuk'awa.
"Kai Musa d'auko kofi in zuba muku kunu ku sha. Farida kin gama miyar tuwanne?" Kamar jiranshi take yi tace.
"Tunda ka bayar da kud'in miyar ba. Ko kuma shekaruna zan siyar in yi cefanen miyar ba."
Musa a guje ya je a kawo kwano da kofuna. Saminu ya zuba musu kunu ya sa musu Alala."
Murja ce ta kawo Aminu kusa da kwanon nashi, har ta juya yace.
"Zo murja ki je ki siyo kayan miya na d'ari,sai ki siyo manja na hamsin, maggin talatin, sai ki d'an karb'o mana kullin bushsshen kifi na d'ari, yau mu d'anji zak'i ko?"  Dubu d'ayar da Aminu ya bashi ya mik'a mata, sai da ta fita ya dubi Farida yace."
"Farida me yasa baki da wani aiki daya wuce ki tsinkani a gaban yarannan. Yanxu bazan iya samun magana me dad'i daga bakinki ba?" Harara ta watsa mishi tace.
"Ai babu wani taushi da zaka iya samu daga gareni, tun safe rabonmu da abinci, amma yanzu daka shigo yaranka ka sani ai. Ni baka bani alalarba bare kunun." Mik'a mata gorar da kwanon yayi, tako sa hannu ta karb'a.
"Ki rage ma Murja nata."
Yaranshi yake kallo yanda su ke cin Alalen kamar nama. Murja ce ta kawo cefanen, canjinshi ta bashi. cikin k'ank'anin lokaci aka gama had'a komai. Tuwon aka kwashe aka xuba a faranti dan ya huce, dan bashi da maraba da talge, iyakar garin kenan a gidan. Sai wajajen bayan isha aka sauke tukunyar miya, d'an ragowar itacen daya saura ta d'aura ruwan wanka.
Murja ta gama yi ma k'annenta shinfid'a a falo, suna zaune akan katifa suna cin tuwonsu. A haka Farida ta shigo ta same su."
"Murja sai da safe, ni kam na gaji kwanciya zanyi. Tana gama fad'ar haka ta shige ciki."

Gadalanci
Aminu
Zaune yake a d'akin da Dada ta koma, Fatin Mami da Zarah har sun yi Bacci, Mardiyya tana waje tana gyara shinkafar masar gobe.
"Aminu shikenan ka dena cin abinci sai kunu Ka yi hak'uri da rayuwa dan Allah ka ji ko? Murmusawa yayi yace.
"Bakin nawa ne babu dad'i Dada. Zama ta gyara tace.

"Ni so nake yi da zai yiwu me zai hana ka koma tsohuwar sana'arka ta sai da kayan gwari, sai ka kafa d'an teburinka a bakin titi, ni bana son dakonnan, dubi fa yanda Abokinka Saminu yanda ya tsofe, in tsufa ya saukar mai jikinshi zai fad'a fa." Aminu ya d'ago kanshi yace.
"Toh Dada nima inata tunanin wacce sana'a zan kama tunda na d'an tara kud'ina. Amma Dada na amshi kud'ad'e a wajan mai adashen gata, sabida hidimar asibitin Hauwa. Dada ta kalleshi rai a b'ace tace.
"Au kai ya dace kenan ka d'auki nauyin Hauwa Aminu? Ina 'yan uwan nata, mijin Hafsa ai mai kud'ine tunda shago gareshi babba a kasuwa na atampopi.
"Ki yi hak'uri Dada, wallahi nine naso in yi mata, dan Jamila ma da Baffa sun so a siyar da gwal d'in ita Hauwan ayi amfani da kud'in toh nine nak'i." Zuchiya ta ja kawai tace.
"Allah ya kyauta, ni kam zan kwanta kuma."
"A tashi lafiya Dada." Mik'ewa yayi ya fita tsakar gida. Mardiyya tana zaune ta gasa tagumi tana tunanin mahaifiyarta, Aminu ya zuba mata idanu cike da tausayawa. Har ya isa gareta bata sani ba, sai da ya dafata.
"Mardiyya karki bari rayuwarki ta yi k'unci, ki bi mahaifiyarki da adda'a Allah ya yafe mata kurakuranta. Maganar Muktar kuma karki sa damuwarshi ta dame ki, akwai zab'in miji da zan yi miki, ina nazari tukunna." Rarrashinta ya dinga yi, har sai da yaga ta yi murmushi, kuma yaga shigewarta d'aki sannan ya fita a gidan zuwa shago a waje.

*TALLAH*
Ina kuke amare uwayen gida kai har ma da ƴan mata? Ko kun san Mrs Bukhari mai kayan ƙamshi, ai in dai batu na kayan ƙamshi gyaran jiki da na ɗaki to kai tsaye ku ne mi Badi'at domin gwana ce ta ko wanne fanni a ciki. "Wai ƙamshi kina nufin Badi'at dai marubuciyar nan tamu mai nishaɗantar da mu?"
"Tabbas Fati ita take magana, ai kin dai ji yadda ake magana a kai na, hatta me gidana ya jinjinawa Badi'at domin duk wani ƙamshi da zaki ji a jikina tare da gidana to daga ita ne, ke me kankat ma har gyara na nake yi domin gyaran aurena daga gareta ne, shi ya sa bana wasa da gyaran jikina da na gidana har kuke kirana da ƙamshi."
"Eh tabbas nima na jinjina mata, kuma zaki bani addireshinta domin nima na kwankwati wannan garaɓasa. Ko zaki iya faɗa mini abubuwan da take sayarwa.?"
"Bari na faɗa miki akwai...

Humra
Kulacca
Sudanese Humra
Kulacca ta gashi.
Turaren wuta ɗan gaske, iri daban daban.
Turaren mopping
Room freshner
Turaren turara kaya.
Turaren wuta na toilet
Sannan akwai ingantaccen maganin infection
Ina da magungunan mata, wanda zai gyara amarya da uwar gida.

Wanda zasu shiga daga ciki kuma
Akwai sabulun amare, da dilka ta amare, wanda zaisa amarya ta fito ta haska tas
Kabbasa
Setin kujerar tsugunno
Sannan inayin turaren wuta da kasko, da ashana wanda ake rabawa a taron biki ko suna.
Ina bayar da sari.

Ma sha Allahu to taya zan sameta domin mallakar nawa?

"Kai tsaye zaki mata magana ta whatsApp ko kiranta ta wannan number.

08179523215

*TALLAH*
A yau nazo muku  da manya manyan magunguna domin gyaran Auranmu! Saboda yadda zamantakewarmu ta AURE keta kara tabarbarewa. Mata iyayenmu ku fito ku gyara jikinku , domin wallahi har Abadan macen da bata gyara bata isa ta hada kanta da mace me gyara ba har abadan! Mu gane yaku yan uwana mata, ma'aurata! wallahi gyara shine mace Akwai mata dayawa dasuka san magunguna na, a online Suna siya kuma Alhmdulillahi ba wadda ta siya bata dawo tamin godiya ba, Alhmdulillahi!Alhmdulillahi! Alhmdulillahi! Yawancin mata dayawa na nemana ta dayan sim dina sede nayi losing dinsa sede wannan shi yake Aiki 08104335144, A YAU NAZO MUKU DA MAGUNGUNA INGANCI DA IZININ UBANGIJI, WATO AINIFIN HADI Iri ~iri na MALLAKA D'ANA MIJI ALFARMAR ANNABI SAW, ina tabbatar muku da magunguna na babu shamaki base na tsaya bata lokaci a bayaniba zanso ku gwada dan tantance GASKIYA * Akwai cututtukan dake hana maganin mata aiki idan kinason sani ki tuntubeni ta wannan lambar 08104335144 wadannan cututtukan inhar kinadasu wallahi duk maganin daza kisha bazeyi Aiki ba, kuma bazaki taba fahimtar komiba a harkar dadih na magungunan mata.

*MUNADA MAGUNGUNA AVAILABLE KAMAR HAKA*👇🏽

*ingantaccen maganin infection *

Ingantaccen maganin basir

Ingantaccen maganin gyaran nono

Ingantaccen maganin gyaran hips

Ingantaccen maganin kara kiba kiyi dumur~mur dake

Ingantaccen maganin rage tumbi  meyi tsakani da Allah

Ingantaccen maganin matsin  farji mesa dadin farji ga azzakarin d’ana miji.

Ingantaccen MALLAKA TA DOMIN ALLAH (Bata harkoki) shine sunansa, hmmmm Wannan magani inada tabbaci a kansa shidin hadine kawai na mallakar d’ana miji akwai komi a cikinsa na mallaka hajiya ki gwada kisha mamaki Alfarmar Annabi SAW.

Se matsin (GAMADIDI) wannan matsi in kikayi amfani dashi har abadan abidina mijinki baze kawo a gaban wata ya mace ba in har ba gabanki bane wannan inada tabbaci a knsa 💯 kuma wadanda suka saya ma sun kara tabbatarmin da kyaunsa na mamaki.

Akwai zallan hadi na amarya

Akwai hadi na uwar gida sarautar mata wannan seat ne akwai komi a cikinsa.

Akwai ingantattun gumba iri iri kamar haka 👇🏽

Akwai gumbar Madara
Akwai gumba me rubutu 🤐
Akwai gumbar kankana
Akwai gumbar giginya (sa megida kuka)
Akwai ingantacciyar gumba me suna (BARIN MAKAUNIYA)
Akwai gumbar hasi
Akwai zallar gumba wadda ita ta rubutuce zallarta zaki ganta baka karki damu Aikin kawai zaki duba 😉
Akwai gumbar gero
Akwai gumbar ridi
Akwai gumbar garin gamadidi  ita ta mallaka ce zallarta.🤐

Akwai tsumi iri iri sunansu sha yanzu magani yanzu 💯👇🏽

Akwai tsumin kankana
Akwai tsumin baure
Akwai tsumin rubutun Ayar Allah
Akwai tsumin kwakwa
Akwai tsumin giginya
Akwai tsumin GORON SUDAN (wannan special ne dan kudinsa ma daban yake)
Akwai ingantattun magunguna na tada shaawah kama daga na turawa har zuwa na Islamic wato namu na gangajiya. Akwaifa maganin maza madam na hausa dana turawa 😉 duk basuda side effects 👌

Akwai rubutun mallaka
Akwai zoben mallaka
Akwai hayakin mallaka

Akwai zani na mallaka
Akwai hadin ci da kaza
Akwai hadin yan shillah
(Muna dafa kaji da yan shillar ma dade sauran abubuwa da dama,)
Akwai dambun nama na mata wanda ke dauke da magungunan sirri na mata mesa tsantsi da laushi da ruwa a farjin mace 😉

Akwai magunguna na ban mamaki wadanda base na rubutasu ba saboda SIRRI 😉
Muna aika magungunan mu kasa kasa gari gari *UWAR GIDA KI GARZAYO QUEN SANAF Islamic chemist kise magunguna na ingantattun ne insha Allahu kin wuce takaicin d'ANA MIJI * direct to me 08104335144 muna sauraron masu shawarwari a kan zaman AURE insha Allahu, amma in knsan baki shirya siyan magungunan jima'i ba na mata ko na maza pls karki kirani.

_Ummu Maheer_
*DINYAR MAKAHO*

_Miss Hajo_
*KHADIJATUL SABREEN*

_Mrs Bukhari_
*ANGULU DAKAN ZABO*

_Ummu Affan_
*SANDAR MAKAUNIYA*

_Mom Islam_
*TSAUTSAYIN TAUNA*

*Ga tsarin yanda biyan yake*

_Guda d'aya 300_
_Guda biyu 500_
_Guda Ukku 700_
_Guda hudu 800_
_Guda Biyar 1k_

Kai tsaye zaku iya turo kuɗinku ta wannan hanya.

0037219728
FATIMA RABIU SUNUSI
StanbicIBTC BANK

Shaidar biya ta nan

0810 433 5144

Masu turo kati MTN ta wannan number.

0702 616 6536

Ƴan Niger zaku turo da naku kai tsaye ta wanna number.

0706 860 6171

*Mun gode da kasancewa da gawurtattu biyar taku na biyu* 🤘🏿

mrs Bukhari ce
[09/12, 19:49] Badi at: GAWURTATTU BIYAR
DAGA ALK'ALAMIN
BADI'AT IBRAHIM
MRS BUKHARI (B4B)

*ANGULU*
*DA*
*KAN ZABO*
9/10

Mu asalin shuwa arab ne. Duk da shuwa sun kasu kashi _kashi, akwai *kawalmee.* sune farare fat_fat, suna da dabbabin kiwo, kuma suna shan madara, basa iya yin aikin wahala sam, masu son jikine sosai. akwai kuma shuwa masu suna *wadel musa* wad'annan kuma, sune bak'ak'e sutuk, suma suna da dabbobi, suna noma, kuma suna son tafiye tafiye, tamkar fulanin tashi. Toh mahaifiyarmu ta had'a duka wannan biyu, mahaifiyarta kawalmee ce, mahaifinta kuma wadel musa ne.
Suna zaune a wani k'auye a cikin maiduguri mai suna KOSHOB'B'E, k'ark'ashin k'aramar hukumar jere ta jihar Borno. su uku kacal iyayensu suka haifa. mahaifiyarmu mai suna Marne, sai mai bi mata ummu kenan asalin sunanta shine Ajidde, sai kuma Nanne, ita kuma sunanta Latifo. Sunayen yare dukkansu aka sanya musu, domun basa jin wani yare sai yarensu na shuwa. mahaifina malam Sada bafulatanin asaline mazauna garin Adamawa cikin k'auyan mayobelwa, cirani ne ya fito da iyayenshi suka yada zango a garin kano, cikin anguwar tarauni, a gidan wani Alh daya ba kakana gadi, sukai zamansu anan gidan. A gidan aka haifi mahaifina, daga nanne Kanana ya kama haya a waje ya mayar da Hauwa kakata can danta raini mahaifina da kyau. shekara biyu ne tsakanin mahaifina da Baffa Junaidu. Mahaifina na da shekara goma sha bakwai mahaifinshi Allah yai mishi rasuwa, sanadin ciwon ciki na dare d'aya, sai wayar gari akayi babu shi. Tun daga wannan lokacin mahaifina suka soma wahala da buga bugar ciyar da

mahaifiyarsu, sukan shiga kasuwa suyi aiki dan samun kud'i. A  haka mahaifina Sada  ya yanke hukuncin fita cirani. Bai yada zango a ko ina ba sai a maiduguri cikin k'auyen Mafa, mai gari shine mai masaukin bak'i, a gidanshi Sada ya sauke a d'akin samarin da suka fito cirani. Suna shiga kasuwar cikin garin Borno ne ranar cin kasuwa, mahaifina ya samu ubangida wanda yake bashi kayan itatuwan turaren wuta, da turarukan binta sudan, da su kafin_ kafin, suna kaiwa kasuwa. Kamar kullum.
Sada na cikin zauren mai gari yana ta zuba kayan itatuwa a cikin buhu, su kuma turarukan mai a cikin k'atuwar robar fenti ya jerasu, abokin fita cin kasuwarshi Sani yace.
"Sada kayi sauri kasanfa in ba duku duku muka fice ba baza mu samu inda ya dace mu baza kayanmu ba, kai sauri. Sada ya d'ago yace."
"Kama mun buhunnan kaji Sani izamun a ka, saimu kama hanya. Sani ya iza mai buhunnan a ka ga nauyi, haka kuma ya d'auki robar fentin turarukanshi a hannu. Suka soma tafiya da duku dukun asuba.
"Sani wannan karon kuma mai ka d'auka zaka siyar ne?" Sani yace.
"Dilka, da kurkum na d'auko wannan karon nifa riba nake bi, shi yasa ban yarda na nace ma d'aukar itace kamarka ba, ko wacce kasuwa da abunda zan d'auka. Dariya Sada kawai yayi ma Sani, suna tafe suna hirarrakinsu, a hanya su kaita had'uwa da abokan ciraninsu, ko wanne cikinsu da buhun abunda zai kai kasuwa a kanshi. Sunyi tafiya mai nisa kafin suka iso titi, motar zuwa kasuwa suka samu suka shiga, dasu da kayan nasu duk a waje d'aya, harda awakai, suna tafe anata hira, Sani ya lura Sada baya magana sam.
"Sada kaddai tunanin wannan yarinyar da kunya ya hana ka tambayi sunanta kake yi, 'yar fara?" Murmushi Sada yayi yace.
"Sani ai da ita nake kwana nake tashi, tayi nisan da banyi zatoba a tunanina, gashi gwarjininta ya hanani tunkararta. Dariya Sani ya kwashe ma Sada dashi, yace."
"Ni kuma yau na yi ma alk'awarin zan tambaya ma sunanta da k'auyansu, tunda kullum a wajanka take siyan itacen Dorot. Baki Sada ya washe yace.
"Da kuwa na gode Sani, dan ina sonta duk da ba lallai ta auri d'an cirani kamata ba. Sani yace.
"Duk matan dake cikin k'auye burinsu guda d'ayane. Su samu saurayin da zai auresu ya fitar dasu daga k'auyansu zuwa birni, abunda ke cikin birnin ne basa sani, balle kai taji a kanon dabo zaku zauna, Kano ai babban garine mai cike da masu arziki 'yan kasuwa dama masu ci a gwamnatin. Ajjiyar zuchiya Sada ya sauke domin abokinshi ya k'arfafa mishi guiwa sosai akan kyakkyawar 'yar shuwan da yake mafarkin mallaka. Da wannan tunane tunanen suka isa kasuwa. Nan kowa ya shiga hada hadar baza kayanshi a inda ya dace. Sani da Sada tare suke zama a gefen wata rumfar mai siyar da su lubban da farce da misik, kayayyakin humra dai. Sun baza kolinsu, kasuwa ta soma d'aukar jama'a sai saye da sayarwa akeyi, 'yan mata kuwa gasunan gungu_ gungu,  sunata fitowa cin kasuwa. ansha kwalliyar janbaki da hoda da gazal, sai rawar kai suke yi a kasuwa, su ne can, sune nan, su sayi wannan su taya wancan. Sada kuwa matane suka rufeshi sai awun itatuwan  turaren wuta suke yi, Sani ma sai ciniki yake tayi, dama duk ranar kasuwa duk abinda suka kasa k'arewa yake yi tas, sabida jama'ar dake zuwa yawa garesu.

Koshab'b'e
Marne tana gaban madubi tana gyara gashinta wanda ta shurb'uneshi da kulacca sai k'amshi

yake yi. Mayafi ta yane kanta dashi tsab, kayan jikinta a kod'e suke amma kuma tsab dasu babu k'azanta a jiki, kuma an turare tsunman kayan da turaren kaya, sannan tabi jikinta ta shafe da humra sai k'amshi take bazawa. Haka ma k'annenta Ajjide, da Latifo, duk suna cikin kwalliya. Fararene su sol sabida mahaifiyarsu farace fat, mahaifinsu kuma bak'ine sosai shi. K'awayan su marne ne suka shigo da Sallama a bakinsu, ko wacce a cikin k'amshi take. Nan suka rankaya zuwa cin kasuwa, suna tafe suna wak'e wak'ensu da yaren shuwa. A bakin titin k'auyensu suka samu motar kaya da zata kai mutane ciyo kasuwa, suma suka shiga.
Sada yana zaune jama'a sun ragu a kanshi sai tunanin Marne yake yi yana murmushi. Sani ne ya dafashi yace.
"Gasu can fa sun shigo kasuwar Sada, ga mutuniyar taka, Sada in dai ta aureka ka more mace, yaranku zasu yi kyau sosai Sada. Bakin Sada ya kasa rufuwa sam sai washewa kawai yake yi. Dubanta yake yi tayi daban a cikin k'awayenta ta fisu kyau da bud'ewar idanu, fatarta sai shek'i take yi a rana. Gabanshine ya shiga dokawa da k'arfi, saurim kawar da kanshi yayi gefe. Cikin harshen fullanci tace.
